

# PRKARIYA

## CI DA GUMI DA KUMA SAFARAR MUTANE

### MENE NE SHI?

**Safarar mutane ya ƙunshisafarar mutane da ɓoye su a cikin gida ba tare da son ransu ba, da nufin ci da guminsu. Ana iya cimm ma hakan ta hanyar tashin hankali ko barazana, ko kuma yaudarar su.**




**Aikin tilas**
Ana tilasta maka yin aiki cikin yanayi mara kyau ba tare da samun damar hutu ba, ko kuma ba a biya ka ba. Mai yiwuwa wanda kake yi wa aiki ya yi maka barazana ko kuma ya zage ka.

**Cin zarafin jima'i**
Ana tilasta maka yin aikin jima'i a cikin gida, ko shiga cikin dangantaka ba a sonka ba. Mai yiwuwa ba za a bar ka ka huta ba, ko ka ƙi wasu abokan ciniki ko ayyuka.

**Tilasta ayyukan laifi**
Domin biyan bashinka ana tilasta maka yin sata ko bara ko aikata laifuffuka, ko safarar ƙwayoyi ko makamai ga wanda kake yi wa aiki.

**Bautar cikin gida**
Kana tsaftace gida da dafa abinci da wanki ba tare da an biya ka ba. Watakila ba ka da wurin kwana mai kyau, ko a ba a barin ka fita daga gidan da kanka.

## Kana da HAƘƘIN a kiyaye ka da kuma damar samun tallafi

**Halin da kake ciki yana iya sauyawa. Abin da kamar zai iya farawa kamar yarjejeniya ta gaskiya zai iya zama abin ci da gumi, musamman idan an yi maka ƙarya game da abin da za ka yi a kan hanya, ko kuma da zarar ka isa inda za ku je.**

### BA LAIFINKA BA NE

Ba za ka taɓa yin laifi ba idan waniya ci da guminka ko idan an tilasta maka aikata wani abu. Kana iya yin magana da mu cikin aminci kuma ba tare da fuskantar wani hukunci ba. Mun yarda da kai.

**Kungiyar Red Cross da kuma Red Crescent za su iya bayarda tallafi na sirri**

BritishRedCross